SACRIFICE 316

## Hadaya Mai Rai

*"Don haka ina rokonku 'yan'uwa, saboda yawan jinkai na Allah, ku mika jikinku hadaya rayayyiya, tsattsarka, abar karba ga Allah. Domin wannan ita ce ibadarku ta ainihi. Kada ku biye wa zamanin nan, amma ku bar halinku ya sāke, ta wurin sabunta hankalinku ɗungum, don ku tabbatar da abin da Allah yake so, wato nufinsa kyakkyawa, abin karba, cikakke kuma."*
Romawa 12:1-2

**Hadayarka.** Wannan gargaɗin da ake yi maka ka mika jikinka a matsayin *"hadaya rayayyiya, tsattsarka"* sau da yawa ana rashin fahimtarsa. Duk da haka, yana da matukar muhimmanci wajen nuna maka hanya madaidaiciya ta kasancewa fiye da Mai ba da gaskiya ga Yesu Almasihu kawai. Aya na farko tana kalubalantar kowane Mai bi ya mika takamaiman hadaya ga Uba Maiduka bayan ceto. Aya na biyu tana ba da umarni game da rayuwa bayan wannan hadaya. Ka mika kai ga Uba Maiduka kowace rana a matsayin bangare na ɗaukar gicciyarka kowace rana, Luka 9:23. Amma, wannan ba shi ne ainihin ma'anar Romawa 12:1 ba. Umarninsa na *"ku mika jikinku"* yana nufin yin sadaukarwa, mika wuya, da cikakkiyar biyayya ga Uba Maiduka *sau ɗaya tak har abada*. Wannan ba ceto ba ne. Ceto ya dogara akan hadayar Almasihu kaɗai. Wannan ɗabam yake. Wannan ita ce hadayarka. Ba hadaya ta kullum ba. Yana nufin ka ba da rayuwarka ga Uba Maiduka ba tare da wata sharaɗi ba kuma har abada a matsayin hadaya mai rai, tsattsarka, kuma abun karba. Kyauta ce na son rai da ka yi wa Uba Maiduka domin ɗaukakarsa da kuma domin ya yi amfani da kai ba tare da wani kuntatawa ba.

**Don me za ka yi wannan hadaya?** Saboda jinkansa ne. Romawa surori 1-11 suna bayyana jinkan Uba Maiduka. Romawa 12:1 yana gaya maka abun da Uba Maiduka yake so ka yi saboda waɗannan jinkai. Romawa 12:2 yana ba ka gargaɗi guda biyu game da rayuwa *bayan* hadayarka. An bayyana babban jinkan Uba Maiduka a cetonka da tsarkake ka a waɗannan surori goma sha ɗaya na farko. Saboda haka, ka mika kanka ga Uba Maiduka. Zai albarkace ka a wannan rayuwa da kuma cikin madawwama. Duk da haka, dalilin da ya dace da hadayarka ba ya a gabanka. Yana bayanka. Kwarin gwiwar ka da ya dace na dogara a kan abun da Uba Maiduka ya riga ya yi. Ka yi tunanin Yesu yana mika maka hannuwansa masu tabon kusoshi yana cewa, "Bayan dukan abun da na yi maka, ka yi Mini wannan." Wannan ce ma'anar Romawa 12:1.

**Don me hadaya sau-ɗaya tak?** Saboda wannan ce ma'anar kalmomin da suke cikin Romawa 12:1-2. Kalmomin aikatou da ke cikin *"kada ku biye wa"* da *"ku bar halinku ya sāke"* a 12:2 suna a sigar lokaci na yanzu. Wannan na nufin ka yi waɗannan abubuwa biyu yanzu kuma ka ci gaba da yin su duk rayuwarka. Amma, aikin kalmar aikatou ɗin cikin *"ku mika jikinku"* a 12:1 ba ya cikin sigar saukakken lokaci na yanzu a Girkanci. A harshen Girkanci, yana nufin aiki guda ɗaya ne tak. Ba ya nufin a ci gaba da yin sa ba. Yana nufin a yi shi sau ɗaya tak har abada. Kebewa ce tabbatacciya na kanka ga Uba Maiduka. Ka mika kanka gare Shi a matsayin hadaya. Romawa 12:1 game da hadayarka ne. Game da kai ne ka ɗora kanka a kan bagadin Uba Maiduka na dindindin.

**Misalai biyu.** Mamaitawar Shari'a 15:12-17 ya ba da misali ga wannan. Bawan Ibraniyawa da aka 'yanta na iya yanke shawarar *da son rai* kuma *dindindin* ya sake bautar da kansa ga maigidansa. Wannan zabin na dangane da tausayin da maigidan ya nuna masa da ya gabata. Kaunar da bawan yake yi wa maigidan nasa ne ya motsa wannan. Na dindindin ne. Ana amfani da allura mai kaifi a huda kunnen bawan domin nuna cewa shi bawan maigidan ne har abada. Wannan bautar ita ce zabin bawan. Ba a tilasta masa ba. Shawara ce na dindindin. Wani misalin kuma yana cikin hadayun dabbobi na Tsohon Alkawari. Dole dabbar ta zama abun karba kafin a ɗora ta a kan bagadi. Dabba mai cuta ko mai aibi ba abun karba ba ce, Littafin Firistoci 1-5. Wannan na kwatanta bangaren tsarki da abin karba na hadayarka ta Romawa 12:1. Mutuwar dabbar hadayar na nuna dindindin ɗin hadayar. Babu dabbar hadaya da ya rarrafe daga bagade sa'ad da ya yi zafi. Babu firist da ya wuce da dabbar a karshen yini domin ya sake mika ta a wata rana. Hadaya ce ta dindindin. Idan ka dauki hadayarka ta Romawa 12:1 daga kan bagade sa'ad da ya yi zafi, to ba ta taba zama hadayar Romawa 12:1 ba.

**Maimaita hadayarka.** Shin ya kamata ka maimaita hadayarka na Romawa 12:1? Eh, idan hadayarka ba abun karɓa ba ce. Hadayar Romawa 12:1 dole ce ta zama mai rai, tsattsarka, kuma abun karɓa. Kana da rai domin, sa'ad da ka gaskata da Almasihu, *"ka riga ka tsere wa mutuwa, ka kai ga rai,"* Yahaya 5:24. Kasancewa a matsayin hadaya tsattsarka alhakinka ne. Dole ne dabbobin Tsohon Alkawari su zama abun karɓa kafin a miƙa su hadaya. Babu dabbar da zai iya zama cikakkiya. Amma dole ne ta kasance ba tare da cuta ba, da lafiya, ba kuma tare da aibi ba. Wannan yana kwatanta abubuwa biyu game da hadayar Romawa 12:1. Na farko, hadayarka dole ne ta kasance babu cuta. Dole ne cutar zunubi da rabuwa da Uba Maiduka a warkar da ita ta wurin ceto. Shi ya sa Romawa 12:1 aka rubuta shi ga Masu bi kaɗai, (kamar yadda kalmar '"yan'uwa" a cikin ayar ta nuna). Hadayar Kafiri ba abun karba ba ce domin dole ne a miƙa ta *bayan* ceto ba *kafin* ceto ba. Dole ne ka zo wurin Yesu kafin ka iya binsa. Don ka tabbatar da cetonka ziyarci www.Gospel316.org. Sashin mai tsarki yana nuna matakin tsabtar ruhaniya mai karɓuwa a rayuwar Mai bi. A lokacin kawai ne hadayarka na Romawa 12:1 za ta zama abun karba ga Uba Maiduka. *"Kowa yă tsarkake kansa daga ayyukan nan kaskantattu, zai zama ma'aikaci mai daraja, tsarkakakke, mai amfani ga Ubangiji, shiryayye ga kowane kyakkyawan aiki,"* 2Timoti 2:21. Ba za ka iya zama cikakke ba. Amma, za ka iya gabatar da kanka a daidai matakin lafiya da tsarki na ruhaniya. Bayan Uba Maiduka ya karɓi hadayarka mai rai da tsattsarka, bai kamata ka buƙatar miƙa ta kuma ba. Amma, idan hadayarka ba abun karɓa ga Uba Maiduka ba domin ta kasance ta ɗan lokaci ko kuma ba tsattsarka ba ce, to sai a bukatu maimaitawar da shi. Ka miƙa kanka a matsayin hadaya ta dindindin, mai rai, da tsattsarka. Da son rai ka mai da kanka bawa ga Uba Maiduka na dindindin. Ka yi wannan a hankali. Yanke shawara mai tsanani sosai ce bayan ceto. Bayan an karbi hadayarka, ka ci gaba zuwa rayuwar Romawa 12:2 wanda ke da rashin biye da canza rayuwa, a matsayin mabiyin Yesu Almasihu na gaskiya. Bayan dukan abun da ya yi maka, ka yi Masa wannan!

**Rayuwa bayan hadayarka.** *"Kada ku biye wa zamanin nan, amma ku bar halinku ya sāke, ta wurin sabunta hankalinku ɗungum, don ku tabbatar da abin da Allah yake so, wato nufinsa kyakkyawa, abin karɓa, cikakke kuma,"* Romawa 12:2. Wannan ayar na ba da gargaɗi game da rayuwa bayan hadayarka ta Romawa 12:1. Waɗannan gargaɗai suna cikin sigar lokaci na yanzu, ma'ana ka ci gaba da kin biye kuma da canza rayuwa ta wurin sabuntawar da hankalinka akai akai. Kada ka biye da, kada ka yarda da, ayyukan zunubi na wannan duniya. Kada ka bari duniya ta siffanta waye za ka kasance a matsayin Mai bi. Romawa 12:2 yana gargaɗinka ka *"bar halinka ya sāke, ta wurin sabunta hankalinka."* Kalmar Girkanci da aka fassara da *sāke* kalmar da Yesu yi amfani da ita ce a Matiyu 17:2 da Markus 9:2 inda aka ce an *sāke kamanninsa.* Romawa 12:2 gargaɗi ne na canza kamanninka ta wurin sabuntawa (gyara, cikakken canji don mafi kyau) hankalinka. Wannan sauyi (mai ban mamaki fiye da yadda kwaro ke zama malam buɗe ido) yana cika yayin da kake koyon da rayuwar Maganar Uba Maiduka. Ka yi hadayarka ta Romawa 12:1. Kada a matse ka cikin yanayin duniya. Ka canza kamanninka yayin da kake koyon da rayuwar Maganar Uba Maiduka. Sa'an nan za ka iya gane ka kuma rayu da nufin Uba Maiduka.

**"Don ku tabbatar da abin da Allah yake so, wato nufinsa kyakkyawa, abin karɓa, cikakke kuma."**

**Romawa 12:2**

---

*Hadaya Mai Rai* © 2026 na John D. Morris III, Ayyukan Manzanni Daya Takwas ne ya buga shi. Kana iya buga shi, kwafa, wallafa, aikawa ta imel, ko aika saƙonsa cikin 'yanci muddin abin da ke ciki bai canza ba kuma an haɗa wannan cikakken bayani. Kana iya hada sunan hidimarka ko ikilisiyarka ko tambarinta a saman shafi na ɗaya, kuma ka kara bayanan tuntubarka a sama da layi mai kauri kusa da kasan shafi na biyu. *Sacrifice316* ya dogara ne ga Littafi Mai Tsarki kaɗai. Ya wanzu domin ya taimaka wa mutane su yi girma a ruhaniya fiye da kasancewa Masu bin Yesu kawai. Kana iya aika wa Ayyukan Manzanni Daya Takwas imel, (da Turanci idan zai yiwu) zuwa: Hello@Mail316.org. www.ChristianLingua.com. ne ya ba da sabis na fassara. *Hadaya Mai Rai* ana samunsa a harsuna 48 kyauta a www.Sacrifice316.org. Ambato a cikinn sigar Turanci daga New American Standard Bible 1995 na The Lockman Foundation ne. Nassosin Littafi Mai Tsarki a wannan fassarar daga: Littafi Mai Tsarki (Sabon Juyi) ne.